BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215 www.bu.edu/Africa/alp africa@bu.edu 617.353.3673

**Interview 5: Isa Sani, Masassaƙi**

Masassaƙi (MSS): Ni sunana Isa Sani. Shekaruna arba'in da biyu, kuma aikin sassaƙa nike yi. Ni na Yamai ne.
Int: Mm.
MSS: Dâ karatu ne nike na boko…
Int: E.
MSS: Na ga karatun bai nan ga yi, na ce sana'a zani kamawa. Shi ya sa ni zo ni shiga aikin ga. A…a wanga aiki sa'ad da ni bar lak… sa'ad da ni bar makaranta ni ce ma ubana ni kawai makarantan yanzu ya ishe ni. Ina da wani abokina Allah ya yi mai cikawa ana ce mai Kindo.

Int: Mm.
MSS: Shi ne ke aiki tare da Garba, ya ce min wānè tun da ba ka dinga zuwa makaranta, ka zo ka… mu je wajen maigidana ka gaya mishi abun ga ɗinka yalla zai ɗauke ka.
Int: Aha.
MSS: Ni ce mishi na san ko na zo bai ɗauke … ni ce a'a mu je dai. Na zo na tambaye shi, na ce a wānè, ni tamabaye shi ni gaida shi, ni ce mishi wane aiki nike so ya ce wane irin aiki. Ni ce ni dai aikin ga nike so. Ya ce a'a. In je in diba kaina ya ba ni sati guda in tai in diba kaina. In diba in aikin hwata nike so in aikin kira nike so in tai dai in diba kaina duk aikin da nike so in zo ya ɗauke ni. Ni ce mishi ni wane ba ko aikin da nike so sai aikin ga. Ya ce mini to shi ke nan in je Lundi in zo in hwara. Shi ne mahwarin shigata aikin ga.

Int: Mm.
MSS: Shi ma nan ya koya.
Int: Ee.
MSS: Dan akwai wani … wani tsoho, shi ne da ya je Maraɗi ya kawo shi ya koya mai.
Int: Ee.
MSS: E. Garba ma ba uwayenshi suka koya mishi ba. Shi ma wani tsohon ne ya tashi nan ga ya tai neman itace dajin Maraɗi.

Int: E.
MSS: Daga nan ne ya ga Garba ya zo shi ya zo shi … ya ka shi nan ga gari ya koya mishi.
Int: E.
MSS: Yanzu ina da shekara ishirin da biyar da nike koyon aikin ga. Ishirin da biyar. Ke nan tun da ni bar lakkol ni zo nan ga. E. Na hwara koya…
MSS: E to icce da nike aiki akwai icce biyu Nij…, na ƙasa ga ne. Akwai wani gudu da ake ce mishi madobiya.
Int: Madobiya.
MSS: Akwai guda ƙirya.

Int: Mm.
MSS: E. Amman akwai kama wanga. Wanga ana ce mishi marke. Marke ko iri biyu ne, akwai marke baƙi akwai marke ja. Wanga marke, iri biyu ne, wanga marke ja ne. Nijar ake samunshi. Amma akwai marke biyu e marke guda wanda ake samu ban a Nijar ne ba. Ana huto da shi wani Tȍgô, wani Bȅnîn, ko wani Gh□nâ. E, ake kawo shi.
MSS: Akwai lokacin da ba mu samun ice, ga damana.

© Boston University

Int: E.
MSS: Ga damana ba mu samun icce yanda muke son shi.
Int: E.
MSS: Dan an yi shibka cikin gonakki, motoci da ke shiga gonakki su zo su ɗauko itacen, in hatsi ya girma ba su da dama… ba su samu hanya shiga hatsin.
Int: E.
MSS: Ke nan cikin damana, muna samun … ba mu samun icce yadda muke sonshi.
Int: Mm.
MSS: Amma aiki ya du ... kullum muna yinshi.

Int: Mm.
MS: E. Akwai modal da yawa da muke yi. Giwaye akwai modal da yawa. Duk, waɗanga duka abunga ne. Wanga macce ce tana da goyo kuma tana da tukunya bisa kanta. E. Wagga ma macce ce tana da goyo *mais* icce ne bisa gare ta. Wagga ko macce ce tana da goyo kuma tana da ɗa bisa cikin hannunta.
Int: Mhm.
MSS: E. To yanzu akwai masu anfani da shi kuma akwai waɗanda ba su anfani da shi.
Int: Mm.
MSS: Masu anfani da shi su ne Turawa. Dan baƙaƙen mutane ba su so su saye shi. Kuma in ka saye ko watà macce hakan ga ka je ka aje gidanka sai a ce kaman kana bauta mishi ne.

Int: E.
MSS: Ka gane? Shi ya sa ba su saya.
Int: E.
MSS: *Mais* yanzu mutane sun hwara ganewa.
Int: Mhm.
MSS: Sun hwara ganewa mu ma da muke yi ado ne muke yi, ke nan yanzu mutane sun hwara ganewa in sun saya su ma su zasu z... zasu tai ne can su yi ado. Amma dâ mutane ba su saya. Ba su saye shi. Wata ran waɗannan da … ka san mu kaman karuwwai ne kuwa abin da ke saye shi ne kake ƙirƙira kullum. Kak ka je ka yi wani sai ya yi sati ko wata ba ka saida ba.
Int: E.
MSS: Ka hi son ka yi abin da da ka yi ha yake kwana ukku ka saida. Amma wata ran ma muna samun, muna da …in kana …cikin kwana ma, kana samun abin da kake so da ka zo sai ka yi shi.

Int: E.
MSS: E. Sai ka yi kaman ka ce to za … zaka gani ka yi wani abu, in ka sa cikin kasuwa yalla yana abunga, yana anfani. To wallahi dâ ne muke samu.
Int: E.
MSS: Yanzu ba mu samu.
Int: E.
MSS: Dan yara ba su son aiki. E. Kuma mu ma da muke cikin aikin ga dai dan ba mu da wani sana'a ne, shi ya sa munka shiga aikin ga. Kam mu je gobe muna tambaya wani.
Int: E.
MSS: Parsike aikin ga da hwarin ma da anka ɗauke shi aikin ga bayu ne ke yin shi. Ka gani? Aka ce wanda duk ba bawa ba ne bai aikin ga.

Int: E.
MSS: Mu muna yinshi ba dan sabo da wani abu ba, dan dai mu samu abin da zamu ci.
Int: E.
MSS: Kâm mu tai mu tsaya gab..e… gab…bisa ga wani mu ce ya ba mu wani abu. Ka gane?
Int: Mhm.
MSS: Don in muna samun, wata ran muna samun abin ga, in muka je tambaya aure ma sai a hana muna a ce mu bayu ne sabo da aikin ga da muke yi. Ka gani?
Int: E.
MSS: Ke nan yara in suka ji labarin nan, ba su son aikin nan.

Int: E.
MSS: Ka gane?
Int: Haka ne.
MSS: …To ka ga dai ga wanda muke hwara yi da shi, wanga. Wanga sunanshi gizago.
Int: Gidago?
MSS: Gizago.
Int: Gizago. E. Wannan kuma sunanshi magagari. Magagari iri biyu ne. Akwai wanga kuma akwai wanga. Duk magagarai ne. CHECK
Int: E.
MSS: E. Waɗannan tun na dâ wannan mun bar lokacinsu yanzu. Sabi ne muke yi. Yanzu sabin kaya ne gare mu.

Int: E.
MSS: Dâ na Katako[1] ne mu …Katako muke zuwa muna sayen kaya. Na Katakon nan ba zasu gyara muna abin da muke so ba. Amma yanzu nasaru su ke ka muna magagari. E. Kamar in nasara ya zo sai in tambai shi in yana da abun ga …kama yana iya ya ka mini magagari sai ya gaya mini 'wane na iya in ka maka dan in taimaka maka' kama taimako ne. E. ka ga dai wanga ice na aka yanka. … Wanga marke ne.
Int: Mhm.
MSS: Icce ne na yanka nan zan yi giwa.

Int: E.
MSS: Giwa ne zani yi. Ke nan yanzu zani hwara forme giwat ku gani yanda take. Yanzu kahin ka…sakamako duka na giwa duk sun hita. Ga kan ga. Ga kunnȅ guda ga wâncân kunnȅ, wânga kuma baya ne.
Int: E.
MSS: Amma kuma sai an yanka.

Int: E.
MSS: Ke nan in lokacinku yana badawa sai in hidda shi.
Int: E.
MSS: Tô, yana ɗokan lokaci .
Int: E.
MSS: *Parce que* hannu gud…mutum guda ke aiki.

[1] This is the name of one of the Niamey city markets, where most hardware and construction goods are found in Niamey. Its name came from the name of construction wood which is 'katako' in Hausa because it is sold there.

Int: E.
MSS: Ke nan wanga giwa in zani hidda shi sai na doki awa … munti talatin. Yana da wuya sosai *parce que* iccen ne ke da ƙarhi. Icce ne ke da …yana da tauri kùwà.
Int: E.
MSS: E. Yana da tauri kwarai. Yanzu giwa da nai, nai, na yi abun ga na hidda sakamako yanzu.
Int: Mm.
MSS: In ba sama ne na je, in ba sama ne na je e bisa abun ga ba, ban iya aiki shi kuma.
Int: E.
MSS: *Parce que* ƙarami ne kuwa.

Int: E:
MSS: Inda babba ne d□ ina iya sassaƙe shi da wanga gizago ha in kare shi.
Int: E.
MSS: Amma inda ƙarami ne in ni ce in sassaƙe shi hakan ga da gizago yana ƙarewa.
Int: E.
MSS: E. Ka san a nan ma in ka zo aikin da kake hwarawa in ka zo shi ne giwa.
Int: Mmmm.
MSS: E. Kama in muka samu wani yaro zamu koya mai aiki, aikinshi na hwarin shi ne giwa.

Int: E.
MSS: Sai ya iya giwa. Sa’annan a koya mai dorina.
Int: E.
MSS: Sa’annan ya hwara shiga wasu aiki.
Int: Aiki.
MSS: E. Amma ba a koya maka …
Int: To ita yin giwat ba ta da wuya ne?
MSS: Tô, tana da wuya. Don akwai yara da muke samu ma ha su yi… shekara ba su iya giwa ba.

Int: Aa?
MSS: Ka san komi sai ka sa… sai ka kwantad da hankalinka. Kuma yara yanzu abin da suke yi, in muna aiki ba su zo su zamna kusa gare mu kama yadda mu manyanmu in suna aiki sai mu zo mu zamna kusa gare su mu ga abin da suke yi.
Int: Mm.
MSS: Su kawai da ka aiki yaro ya tai ya dawo, sai ka ga ya shiga sha’aninshi. Ya kamata yaro in ya ga maigidanshi yana aiki ya zo ya zamna kusa gare shi, ya ga abin da yake yi sabo da gobe. Ka gani? To su ba su yi. …Yaro in ya yi shekara bai iya giwa, ai bai iya komi ba. Wannan ko makaranta anka sa shi ma bai gyara komi.

Int: Mm.
MSS: Yanzu ga ya nan na hidda kai. Yanzu ina son in hidda hannu …hannun giwa. Yanzu ga ya nan na hidda kai, na hidda hannun giwa. Yanzu za ni gyara kunnuwa. Ga ya nan yanzu kunnȅ guda ya hita.
Int: Mhm.
MSS: …. Yanzu bayan ne za ni huddawa. Bayan gi …bayan giwa. Yanzu za ni gyara baki. Yanzu ƙahwahuwa ne zani huddawa. Giwa hwa ta hwara zowa ko?
Int: Mhm. Ya yi kyau. Mhmhm.

MSS: Dan dai… dan dai abunga ne, dan dai a gwada muka sakamako ne. Da inda son samu ne inda ba jiya ne da ni yi aiki na gaji, da na so in yi muku babban macce. Ka gane? *Mais* jiya na sha aiki, na gaji. Yanzu ma hannuwana suna ciwo ƙwarai kùwà sabo da aikin da na yi jiya.
Int: Aikin mai wuya ne.
MSS: Mai wuya ne. E. Da na so in yi babb…babban abu ne na so in yi guda in gwada muku. To kwam na kaji ya kamata ai e… sai dai radda Allah ya kai mu hakanga in kuka zo… Yanzu zan raba kunnuwa da kai ne kùwà.

Int: Mm.
MSS: Ka gani? Ke nan kan … kunne ya hita da kai.
Int: Mm.
MSS: Na wajen kuma, sai na raba su. Yanzu ta hwara giwa.
Int: Mm.
MSS: Yanzu hannun ne za ni huddawa. Sai an yi kai, e. Sai an yi kai tukuna. Kwan kḕ ƙarami ne sai an yi kai.

Int: Mm.
MSS: Inda babba ne da baya muke hwarawa sai mun samu baya tukuna, mun samu ƙahwahuwan sai mu yi, yanzu zamu hidda kai.
Int: Mm.
MSS: Kuma mu ba wani zane muke ba.
Int: Mm.
MSS: Wasu sai sun yi zane. Kama su ɗauki iccen sai sun zana wani abu bisa gare shi sa'annan su hwara aiki.

Int: Mm.
MSS: A'a. Mu da ka ɗauki aiki, model din, abun ɗin yana bi …cikin kanka. Da ka ɗauki icce ka san mi ye zaka yi shi.
Int: Mm.
MSS: Kayan aikinmu ne duk sun lalace.
Int: Mm.
Int: Kuna samun matsala wajen kayan aiki?
MSS: Wallai. Sosai muke samu. Wata ran ka zo kana so ka yi aiki, babu kayan aiki.

Int: Mm.
MSS: Dole sai ka zamna. Waɗanda ke ka min kayan aiki yanzu sun bar ka muna. Su ma kayan aiki yanzu sun yi tsada. Ko kana so ka saya ba ka iya saya. Sai ka aje kuɗi sosai, sa'annan ka samu ka sai kayan aiki. In ka saye ba yana daɗewa ne ba, dan dai ka sami kwana biyu ko kwana ukku kana aiki, ha yake lalacewa. To da…do…da abunga …kayan aiki guda muke anfani amma yanzu kowa da nashi.
Int: Mm.
MSS: To ka ga ko abin yana zama reni, abincink…abokinka ya sai kayan aiki ka ce ya ba ka ka yi aiki, kana samun kuɗi. Ya kamata ji ciwon kanka kaima ka je ka yi ma kanka.

Int: Mm.
MSS: Yanzu ga giwa …ga ta nan ta kare man. Ka ga wanda magagarin ne za ni … sai na goge shi tukuna. Da magagari. Magagari iri-iri ne.

Int: Mm.
MSS: Ka gani? In ni sa wanga, in ni ƙare sawa wanga, akwai guda da ake sawa, shi ne wanga. Shi mai sulbi ne. Shi ne nike sa. Ka ga ya hwara sulɓi ko?
Int: E.
MSS: Ka gani?
Int: E.
MSS: Wanga ake sa. Shi ne ake sa, a hwara. In hwara goge shi. E. Shi ne man ɗin shi ne ake sawa. Ka ga ga mai shi ne da ake sawa. Yanzu ba ta ƙare ba. Ba ta yi walƙiya. Ba ta iya walƙiya yanzu dan ba a ida aiki ba.

Int: Mm.
MSS: E. Daga baya ne in ni ƙare wanga, in ni ƙare sa'annan ne za ni yi mata idanu.
Int: Mm.
MSS: Kuma da abun ga. Ke nan in ni zana idanu, …. Yanzu haure ne nike na ga yi, wajen haure ne nike nan ga yi.
Int: Mm.
MSS: Icce muke sawa. Hwarin icce. E. In, in iccen, in iccen baƙin icce ne ke nan hwarin icce ne ake sawa dan a ga idanun. Kaman ci, e, baƙi, hwari yana cikin baƙi ana ganinshi.
Int: E.
MSS: E. In jan icce ne ana sa baƙin dan kama ja yana cikin baƙi, ana ganinshi. E. *Mais* haƙuran ga da muke sa musu, haƙuran ga, abunga ne eeee ƙashin, ƙashin raƙumi ne.

Int: Mhm.
MSS: E. Ƙashin raƙumi ne. Da haƙorin da muke sa, na giwa muke sawa. Amma yanzu aka yi intardi aikin, aikin abunga, hauren giwa, yanzu in muke aiki, *parce que* nasaru ma in sun ziza su tambaya, Bato …Bature in zai saya, zai tambaya, sai ya tambaya hauren na mine ne? Sai mun gaya mishi aaa na raƙumi ne. E. Ƙashin raƙumi ne. Sa'annan suke saya.
Int: Mhm.
MSS: E. Ke nan ƙashin ga da da nike sawa na … ƙashin raƙumi ne. E. Wata ran ko abunga muke zuwa, Kasuwa Ƙasa (a market in Niamey), in aka ci malku, mu kwashe ƙassasuwa mu zo mu yi aiki da su.
Int: Mm.
MSS: E.